# Gwaji na Tsarin Shirin Matasa na PYD

| FALLAYEN TAKARDUN KARATU | KAYAN AIKI |
|---|---|
| • Tsarin Shirin Matasa na PYD (duba shafi na 2) da aka sake ƙirƙira a kan Fallen takardar rubutu. | • Fallen takardar rubutu<br>• Makar rubutu<br>• Karamar takardar ɗaukar bayanai (launi 2) |

**Lokaci:** takriban masaa 2.

**Manufa:** tathmini jinsi mradi wako unahusisha vijana kwa sasa katika mradi wako wa P/CVE,unganisha shughuli zinazoendelea/zilizopo kwa vipengele vya PYD, na utengeneze shughuli zilizorekebishwa au mpya zinazokuza PYD.

## Matakan Aiwatarwa:

1. Ɗaiɗaikunku ko a cikin rukuni, ku yi tunanin sakamako ɗaya da kuka gano a furojet ɗinku na P/CVE da ya dama da matasa ko ya yi tasiri gare su sannan ku rubuta shi a fallen rubutunku.
2. Ku rubuta ayyukan da kuka shirya a ƙarƙashin wannan sakamako, kowane aiki a kan mabambantan ƙananan takardun ɗaukar bayanai. Ku ɗora waɗannan ayyuka a wurinsu da ya dace a kan tsarin.
   a. Alal misali, ko kun shirya wata horaswa ga matasa game da ƙwarewar sadarwa da tattaunawa? Ku kai waɗannan takardun ɗaukar bayanai cikin akwati na aikin "gina ƙwarewa" da matakin shirin "ɗaiɗaiku".
3. Da zarar kun kai dukkan ayyukan da ke da bayyanannen wuri a tsarin, ku yi tunani game da waɗannan tambayoyin da ke biye (za ku iya yin wannan a ɗaiɗaikunku ko a cikin rukuni):
   a. Ko akwai sigogin PYD ko matakan shirin da furojet ɗinku bai ainihin duba ba waɗanda za su zama masu alfanu a mayar musu da hankali a yanzu?
   b. Ko kuna iya tunanin wasu sauye-sauye ga ayyukan da ake da su ko sababbin ayyukan da za ku iya yi domin ƙarfafa haɗakar PYD a cikin shirinku na P/CVE?
4. Ku rubuta bitoci ko sababbin ayyukan da kuke ba da shawara a kan ƙananan takardun ɗaukar bayanai masu launi daban-daban sannan ku ƙara su a cikin tsarin.
5. Ku bayar da rahoto a matsayin rukuni game da sababbin ayyuka ko waɗanda kuka yi bita sannan ku yi yarjejeniya a kan matakai na gaba na shigar da su a cikin furojet ɗinku.

## Muhimman Batutuwa:

- A ƙarshen aikin, za ku jera sababbi ko ayyukan da aka yi bita waɗanda ake sa ran furojet ɗinku zai iya shigar da su. Ku tabbata kafin ku bar ɗakin, kun gano matakai na gaba na nan take:
  - Tuntubar mutanen da ke wajen ɗakin (kamar abokan hulɗa, matasa, masu amfana, masu tallafawa) domin samun haske ko inganta tunani?
  - Biyo wa da yin taro domin duba kasafi da tasirin waɗannan sauye-sauye?
- Za ku ɗauki hotunan Fallen rubutu da/ko ɗaukar bayanan ayyukan da kuka rubuta da bitoci/ƙare-ƙaren da aka yi musu.

## Tsarin Shirin Matasa na PYD

### **Tushe:** Kwasan-kwasan Intanet na USAID domin Ci Gaban Matasa (PYD)

Wannan tsarin an shirya shi ne bisa ga takardar rubutu da aka yi amfani da ita a Kwasa-kwasan Intanet na USAID PYD, wadda ita ma aka zana ta a kan Misalan Ayyukan Shirin Ci Gaban Matasa da aka Daidaita da Sigogin PYD, da aka Shirya ga Ra'in Zamantakewar Al'umma wadda YouthPower suka samar.

**BAYANIN KUNGIYAR DA AKE HANGE:**
**SAKAMAKO:**

| SIGOGIN PYD | MATAKAN SHIRI | | | |
|---|---|---|---|---|
| | Ɗaiɗaiku | Na mutane daban-daban | Al'umma | Kasa / Tsari |
| **GINA KWAREWA** | | | | |
| **SHIGA DA BA DA GUDUMMUWA** | | | | |
| **ALAKA DA DANGANTAKA MAI KYAU** | | | | |
| **DAMAWA DA ZAMA MAMBA** | | | | |
| **WURARE MASU KARIYA** | | | | |
| **AL'ADU, TSAMMANI, DA TUNANI** | | | | |
| **SAMUN DAMA ZUWA GA SHEKARUN DA SUKA DACE, AYYUKAN DA SUKA DACE DA MATASA** | | | | |